# Babu wani ma'abocin zinare ko azirfa, da ba ya bada haƙƙinsu daga garesu, sai a ranar alƙiyama ya kasance za'a ƙerasu a siffar alluna na wuta

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Babu wani ma'abocin zinare ko azirfa, da ba ya bada haƙƙinsu daga garesu, sai a ranar alƙiyama ya kasance za'a ƙerasu a siffar alluna na wuta, sai a ƙona shi a kansu a cikin wutar Jahannama, sai a yi wa sasanninsa da goshinsa da bayansa lalas, duk lokacin da suka ƙone sai a dawo da su, a cikin wani yinin da gawargwadansa shekara dubu hamsin ne, har sai an yi hukunci tsakanin bayi, sai yaga hanyarsa, ko dai zuwa aljanna ko kuma zuwa wuta".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bayyana nau'ika na dukiya, da sakamakon wanda bai bada zakkarsu ba a ranar alƙiyama, daga cikinsu: Na farko: Zinare da azirfa da abinda ke cikin hukuncinsu na dukiyoyi da hajoji na kasuwanci, shi ne abinda zakka ta wajaba a cikinsa bai bayar ba, idan ranar alƙiyama ta zo za'a narka su aƙerasu akan siffar alluna, kuma a kunna wutar Jahannama a kansu, a yi masa azaba da su, sai a yi wa sasanninsa da goshinsa da bayansa lalas da su, duk lokacin da suka yi sanyi sai a dawo da ƙunarsu, zai kasance a wannan halin na azaba tsawon ranar alkiyama wanda gwargwadan yininta shekara dubu hamsin ne, har sai Allah Ya yi hukunci tsakanin halitta, sai ya zama daga 'yan aljanna ko daga 'yan wuta. Na biyu: Wanda ya mallaki raƙuman da ba ya bada farillar zakkarsu da kuma haƙƙinsu, daga ciki (akwai) tatsar nonansu ga wanda ya zo nema cikin miskinai, za'a zo da waɗannan raƙuman masu girma masu ƙiba kuma mafi yawa kan yadda suke a cikin adadinsu, za'a shinfiɗa shi a jefa shi a miƙar da mai su ranar alƙiyama akan wata ƙasa mai yalwa miƙaƙƙiya, zasu dinga takashi da ƙafafunsu, kuma zasu dinga cizonsa da haƙoransu, duk lokacin da na ƙarshensu ya wuce akansa za'a dawo da na farkonsu a kansa, zai zarce akan wannan halin na azaba tsawon yinin alƙiyama wace gwargwadan yininta shekara dubu hamsin ne, har sai Allah Ya yi hukunci tsakanin halitta, sai ya zama daga 'yan aljanna ko daga 'yan wuta. Na uku: Wanda ya mallaki shanu da tumakai - wadanda suke tunkiyoyi da awakai - waɗanda mai su ba ya bada zakkarsu ta wajibi, za'a zo da su mafi yawan abinda da suke akai na adadi ba za'a tauye komai ba daga garesu, sai a shinfiɗasu a jefa shi kuma a miƙar da mai su a ranar lahira akan ƙasa mai yalwa madaidaiciya, babu wasu masu lanƙwasasshen ƙaho, ko waɗanda ba su da ƙahon, ko masu karyayyen ƙaho, kai su akan mafi cikar siffofinsu ne, sai su soke shi da ƙahonhunansu, kuma su taka shi da ƙafafuwansu, duk lokacin na ƙarshensu ya wuce a kan shi sai a dawo da na farkonsu. Zai ci gaba akan wannan halin na azaba tsawon yinin alƙiyama wacce gwargwadan

yininta shekara dubu hamsin ne, har sai Allah Ya yi hukunci tsakanin halitta, sai ya zama daga 'yan aljanna ko daga 'yan wuta. Na huɗu: Wanda ya mallaki dawakai, su dawakai nau'i uku ne: Na farko: Su laifi ne gare shi, shi ne wanda ya riƙesu dan riya da alfahari da kuma yaƙar ma'abota Musulunci. Na biyu: Su sutura ne gare shi, shi ne wanda ya riƙesu dan yin yaƙi a tafarkin Allah, sannan ya kyautata musu da ciyar da su da ragowar ɗawainiyarsu, daga cikinsu (akwai) barbarar namijinsu. Na uku: Su lada ne gare shi, shi ne wanda ya riƙesu dan yin yaƙi a tafarkin Allah ga ma'abota Musulunci, su a cikin ciyayinsu da dausayinsu dan yin kiwo, to ba abinda zasu ci sai an rubuta masa kyakkyawa adadin abinda suka ci, kuma an rubuta masa kyakkyawa adadin torosonsu da fitsarinsu, ba'a yanke igiyarsu ba, ita ce igiyar da ake ɗauresu a cikinta, suka yi gudu kuma suka yi sukuwa a ƙasa maɗaukakiya; sai Allah Ya rubuta masa kyakkyawa adadin gurabensu da torosonsu, kuma ma'abocinsu bai wuce ba akan wata ƙorama sai su sha daga gareta kuma ba ya nufin ya shayar da su, sai Allah Ya rubuta masa kyakkyawa adadin abinda suka sha . Sannan aka tambayi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi game da jakuna shin su irin dawakai ne? Sai ya ce: Shar'antawa bai sauka ba a sha'aninsu sai dai wannan ayar wacce irinta kadan ne, ita mai gamewa ce ga dukkan nau'ikan ɗa'a da saɓo; ita ce faɗinSa - Maɗaukakin sarki -: {Wanda ya aikata kwatankwacin ƙwayar komayya na alheri zai gan shi, wanda yaaikata kwatankwacin ƙwayar komayya na sharri zai ganshi}. [al-Zilzalah: 8], wanda ya yi aiki a cikin mallakar jakai dan yin ɗa'a zai ga ladan hakan, idan kuma ya aikata saɓo to zai ga uƙubar hakan, kuma wannan mai ƙunsar dukkan ayyuka ne.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6611